# Surah 81: Al-Takwir - سورة التكوير

بسم الله الرحمن الرحيم

[81:0] Bismi ***ALLAH***, Alrahman, Alrahim.*

إِذَا ٱلشَّمْسُ كُوِّرَتْ ﴿١﴾

[81:1] Idan aka mirgina rana

وَإِذَا ٱلنُّجُومُ ٱنكَدَرَتْ ﴿٢﴾

[81:2] Taurari suka rugurguje cikin juna

وَإِذَا ٱلْجِبَالُ سُيِّرَتْ ﴿٣﴾

[81:3] Aka shafe tsaunuka.

وَإِذَا ٱلْعِشَارُ عُطِّلَتْ ﴿٤﴾

[81:4] Aka daina haifuwa.

وَإِذَا ٱلْوُحُوشُ حُشِرَتْ ﴿٥﴾

[81:5] Aka tattara dabbobin daji.

وَإِذَا ٱلْبِحَارُ سُجِّرَتْ ﴿٦﴾

[81:6] Aka jinna wa tekuna wuta.

وَإِذَا ٱلنُّفُوسُ زُوِّجَتْ ﴿٧﴾

[81:7] Aka mayar da rayuka a jikinsu.

وَإِذَا ٱلْمَوْءُۥدَةُ سُئِلَتْ ﴿٨﴾

[81:8] An tambayi yariyan da aka binne da rai:

بِأَىِّ ذَنۢبٍ قُتِلَتْ ﴿٩﴾

[81:9] "Saboda wane laifi ne aka kashe ta?"

وَإِذَا ٱلصُّحُفُ نُشِرَتْ ﴿١٠﴾

[81:10] An bayyana takardun ayyuka (*ga masu su*).

وَإِذَا ٱلسَّمَآءُ كُشِطَتْ ﴿١١﴾

[81:11] Aka kuma shafe sama.

وَإِذَا ٱلْجَحِيمُ سُعِّرَتْ ﴿١٢﴾

[81:12] Aka kunna wutar Jahim.

وَإِذَا ٱلْجَنَّةُ أُزْلِفَتْ ﴿١٣﴾

[81:13] Aka gabatar da Aljannah.

عَلِمَتْ نَفْسٌ مَّآ أَحْضَرَتْ ﴿١٤﴾

[81:14] Kowane rai za ta san abin da ta kawo.

فَلَآ أُقْسِمُ بِٱلْخُنَّسِ ﴿١٥﴾

*Manzon Allah Na Wa'adi*

[81:15] Na rantse da taurarin matafa.

ٱلْجَوَارِ ٱلْكُنَّسِ ﴿١٦﴾

[81:16] Suna guduwa a daidan kewayar falakinsu.

وَٱلَّيۡلِ إِذَا عَسۡعَسَ ١٧

[81:17] Da dare idan ta fada.

وَٱلصُّبۡحِ إِذَا تَنَفَّسَ ١٨

[81:18] Da safiya idan ta buso iska.

إِنَّهُۥ لَقَوۡلُ رَسُولٖ كَرِيمٖ ١٩

[81:19] Lalle ne, wannan maganar wani manzo ne mai daraja.

**81:19 Tarin lambobin surah, da lambobin ayah, da nauyin abjadin sunan “Rashad” (505), da nauyin abjadin “Khalifa” (725), zai ba mu jimlar 1330, 19x70. Wannan ya ba mu hujja sifran riyadiyan Alqur’ani cewa wannan manzo da aka ambata shi ne Rashad Khalifa.*

ذِي قُوَّةٍ عِندَ ذِي ٱلۡعَرۡشِ مَكِينٖ ٢٠

[81:20] Mai ba da izni mamallakin Al'arshi, shaidar qarfafawa.

مُّطَاعٖ ثَمَّ أَمِينٖ ٢١

[81:21] Wanda ake yi wa da’a da amincewa.

وَمَا صَاحِبُكُم بِمَجۡنُونٖ ٢٢

[81:22] Kuma abokinku ba mahaukaci ba ne.

وَلَقَدۡ رَءَاهُ بِٱلۡأُفُقِ ٱلۡمُبِينِ ٢٣

[81:23] Ya gan shi a cikin sararin sama mabayyani.

وَمَا هُوَ عَلَى ٱلْغَيْبِ بِضَنِينٍ ﴿٢٤﴾

[81:24] Bai boye kowane labari ba.

وَمَا هُوَ بِقَوْلِ شَيْطَٰنٍ رَّجِيمٍ ﴿٢٥﴾

[81:25] Kuma ba maganar wani shaidanin da aka la'ana, ba ne.

فَأَيْنَ تَذْهَبُونَ ﴿٢٦﴾

[81:26] Shin, yanzu ina za ku tafi?

إِنْ هُوَ إِلَّا ذِكْرٌ لِّلْعَٰلَمِينَ ﴿٢٧﴾

[81:27] Wannan ba kome ne ba illa zikiri ga dukan talikai.

لِمَن شَآءَ مِنكُمْ أَن يَسْتَقِيمَ ﴿٢٨﴾

[81:28] Ga wadanda suke so tafi a miqe sosai.

وَمَا تَشَآءُونَ إِلَّآ أَن يَشَآءَ ٱللَّهُ رَبُّ ٱلْعَٰلَمِينَ ﴿٢٩﴾

[81:29] Kuma kome kuka nufa daidai ne yake da nufin ***ALLAH***, Ubangijin halitta.